# Surah 96: Al-Alaq - سورة العلق

بسم الله الرحمن الرحيم

[13:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

اقْرَأْ بِاسْمِ رَبِّكَ الَّذِي خَلَقَ ﴿١﴾

[13:1] Yi karatu, da sunan Ubangijinka, wanda Ya yi halitta.*

**96:1-19 daga surori 96 zuwa 114. Surorin farko da aka saukar (96: 1-5) kalmominsu na Larabci 19 ne, haruffansu 76 (19x4). Kuma Suran ta qumshi ayoyi 19 da haruffan Larabci 304.*

خَلَقَ الْإِنسَانَ مِنْ عَلَقٍ ﴿٢﴾

[96:2] Ya hahitta mutum daga tayi.

اقْرَأْ وَرَبُّكَ الْأَكْرَمُ ﴿٣﴾

[96:3] Yi karatu, kuma UbangiJinka shi ne Mafi daukaka.

الَّذِي عَلَّمَ بِالْقَلَمِ ﴿٤﴾

[96:4] Wanda Ya koyar ta hanyan alqalami.

عَلَّمَ الْإِنسَانَ مَا لَمْ يَعْلَمْ ﴿٥﴾

[96:5] Ya koya wa mutum abin da bai sani ba.

كَلَّآ إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لَيَطْغَىٰٓ ٦

[96:6] Lalle ne, mutum yana girman kai.

أَن رَّءَاهُ ٱسْتَغْنَىٰٓ ٧

[96:7] Idan ya kasance mawadaci.

إِنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلرُّجْعَىٰٓ ٨

[96:8] Zuwa ga Ubangijinka makoma take.

أَرَءَيْتَ ٱلَّذِى يَنْهَىٰ ٩

[96:9] Shin, ka ga wanda ke hana,

عَبْدًا إِذَا صَلَّىٰٓ ١٠

[96:10] Bawa daga yin sallah?

أَرَءَيْتَ إِن كَانَ عَلَى ٱلْهُدَىٰٓ ١١

[96:11] Shin, bai fi zama masa alheri ba ya kasance a kan shiriya?

أَوْ أَمَرَ بِٱلتَّقْوَىٰٓ ١٢

[96:12] Ko ya yi umurni da taqawa?

أَرَءَيْتَ إِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰٓ ١٣

[96:13] Idan ya qaryata, kuma ya juya baya.

أَلَمْ يَعْلَم بِأَنَّ ٱللَّهَ يَرَىٰ ﴿١٤﴾

[96:14] Bai san cewa ***ALLAH*** Yana gani ba?

كَلَّا لَئِن لَّمْ يَنتَهِ لَنَسْفَعًۢا بِٱلنَّاصِيَةِ ﴿١٥﴾

[96:15] Lalle ne, idan bai bari ba, za Mu dauke shi ta gashin makwarkwada.

نَاصِيَةٍ كَٰذِبَةٍ خَاطِئَةٍ ﴿١٦﴾

[96:16] Makwarkwadan da yake na kafirci da zunubi.

فَلْيَدْعُ نَادِيَهُۥ ﴿١٧﴾

[96:17] Sai ya kira mataimakansa mu gani.

سَنَدْعُ ٱلزَّبَانِيَةَ ﴿١٨﴾

[96:18] Zã Mu kira zabaniyawa masu tsaron wuta.

كَلَّا لَا تُطِعْهُ وَٱسْجُدْ وَٱقْتَرِب ۩ ﴿١٩﴾

[96:19] Kada ka bi shi; Kuma ka yi sujadah, ka kuma nemi kusanta (zuwa *ga Ubangijinka*).